RESOLVE NETWORK

TAKARDAR BAYANI

# AMFANI DA HOTON BAYANIN MUTANE A MATSAYIN HANYAR GUDANAR DA BINCIKE:

## ƊAUKAR DARRUSA DAGA BINCIKE GAME DA TASHIN HANKALI DA SAKE SAMAR DA HAƊIN KAI A JAMHURIYAR AFIRKA TA TSAKIYA

Wannan takardar bayanin na abatar da dabarun gudanarwa domin dubawa waɗanda aka samo daga binciken da aka gudanar domin rahoton RESOLVE Network, "*Fargaba, Tashin Hankali Kariya da Sake Samar da HaɗinKai: Ɗaukar darrusa daga Labaran Tashin Hankalin Matasa a Jamhuriyar Afirka ta Tsakiya*," na Pauline Zerla. Kari a kan fitattun hanyoyin tattara bayanai kamar su hira da tsararriyar tattaunawa cikin tawaga, yayin tattara bayanan wannan rahoton an yi amfani da dabarar ɗaukar hotunan bayanai daga mutanen da suka tsinci kansu cikin damuwa. Amfani da hotunan bayanan mutane—hotunan da ke wakiltar rayuwar mutane tare da nuni ga abubuwan da suka fuskanta a rayuwa— a cikin bincike zai ba da dama ga mutane su yi tunani game da yanayin damuwa da zasu iya shiga ta tsarin mara magana. Lura da alamun dacewar wannan dabarar tattara bayanai a binciken da za a gudanar nan gaba dangane da tashe-tashen hankula da sake samar da haɗin kai da lamarin lafiyar ƙwaƙwalwa da fargaba, wannan takardar bayanin ta kawo taƙaitaccen bayani game da dabarun amfani da wannan tsari tare da fatan waɗansu ma za su ɗauki hannu domin yin amfani da ita a matsayin tasu.

Domin ƙarin bayani, a duba: Zerla, Pauline. *Fargaba, Kiyaye Tashin Hankali da Sake Samar da Haɗin Kai: Ɗaukar darrusa daga Labaran Tashin Hankali na Matasa a Jamhuriyar Afirka ta Tsakiya*. RESOLVE Network, 2024.

## NAZARIN YIWUWAR AMFANI DA DABARAR

**Amfani da hotunan bayanan mutane—dabarar da ta samo asali daga Afirka ta Kudu, Amurka ta Kudu, da Caribbean—ya dace sosai** wajen tattara bayanai ko gudanar da tsararriyar tattaunawa cikin tawaga da ke mayar da hankali kan halayyar rayuwa da mahalarta taron suka fuskanta. Hotunan bayanan mutane sun fi isar da saƙo yadda ya kamata yayin da mahalartar sun samu damar tattauna hotunan.

**Hotunan bayanan mutane na damƙa akalar tattara bayanai a hannun mahalarta—yana ba su damar** bayyana abin da suke da nitsuwar bayyanawa ba tare da takurawa ko takunkumin yanayin gudanar da bincike ba. A aikace, hotunan bayanan mutane na samar da wani tsari na samun bayanai daga mahalarta tare da mayar da hankali kan abubuwan da suka faru da su a rayuwarsu. Ta bin wannan hanyar, yana iya tasiri a kan shirin samar da zaman lafiya da auna mizanin nasarar shiri, wanda ya dace da tsarin shirin samar da zaman lafiya a karkara.

**Bayan aikinsa a matsayin hanyar gudanar da bincike, ana iya amfani da hotunan bayanan mutane a matsayin dabarar sanya idanu da auna mizanin nasara,** da kuma nazartar lamuran da suka shafi shirin inganta lafiyar ƙwaƙwalwa da tallafi a zamantakewa da shirin samar da zaman lafiya.

## NAZARIN ALFANUN DABARAR

**Wannan tsaɓin dabarar gudanar da bincike na ba da damar fara tattauna tsauraran tambayoyi** waɗanda ke da muhimmanci ga nazarin tashe-tashen hankula. Sannan tana samar da waɗansu hikimomin da masu bincike ba su yi tsammani ba. A CAR, dangantakar da ke tsakanin rasa matsugunai da sake samar da haɗin kai na da yawa. Nasarar amfani da dabarar hotunan bayanan mutane ya danganta ga shirin da aka yi da ɗaukar hannu da kuma aiwatarwa.

**Haɗakar dabarun gudanar da bincike, kamar wanda aka yi amfani da shi a CAR na ba wa bincike damar nazartar waɗansu yanayin damuwa** yayin samar da yanayi mai aminci ta hanyar amfani da hotunan bayanan mutane. Ta hanyar zana abubuwan da suka gabata, wurare, da abubuwan da suka faru, mahalarta na nuna tasirin fargaba da tashin hankali a kan rayuwarsu ta yau da kullum. Wannan na samar da sauyi game da nazartar tasirin damuwar da tashin hankali ya haifar a kan mutane da karkararsu.

**Hotunan bayanan mutane na ba da damar tattauna abubuwan da suka wuce da abubuwan da aka gudanar ba tare da gindaya takunkumin** lokaci ba. Sau da dama waɗanda suka fuskanci damuwa suna da ƙalubalen zamantakewa sannan magance waɗannan ƙalubale ta hanyar mayar da hankali kan abubuwan da suka fuskanta a rayuwa da abubuwan da ke zukatansu a maimakon mayar da hankali kan wani ƙayyadadden lokaci, yana taimaka wa tsarin. Hotunan bayanan mutane na ba wa masu bincike damar mayar da hankali kan keɓantattun labarai na mahalarta sannan damar gudanar da lamarin cikin sigar da ake so na ƙara ƙarfafa shi.

# NAZARIN IYAKOKIN DABARAR

**Hotunan bayanan mutane dabara ce mai inganci wajen binciken labaran ɗaiɗaikun mutane, amma duk da haka ba ta kasance mafita sha-kundum ba. A CAR,** binciken ya gano cewa, hotunan bayanan mutane ya fi dacewa da waɗansu rukunoni. A misali, dabarar ba ta kasance mai jan hankali ba ga manyan maza, sannan a wasu lokuta, sukan ɗauke ta a matsayin wadda ba ta dace ba. A waɗansu mahalli, al'adun zamantakewa na hana amfani da hotunan bayanan mutum ga waɗansu rukunonin mutane.

**Yayin da ya kasance waɗansu al'ummomi sun fi samun damar amfani da hotunan bayanan mutum kamar waɗanda** ba su nitsu da yin magana ko rubutu ba, duk da haka tana tattare da nata ƙalubale. A CAR,waɗansu mahalarta sukan kasance cikin takatsantsan da sha'anin zane yayin da waɗansu kuma suke jin su a takure game da sanya bayanai a kan hotunansu yayin tattaunawar. Ya kamata taron bita game da hotunan bayanan mutane su kasance waɗanda za a iya sauyawa a kowane lukaci sannan masu aminci kasancewar waɗansu mahalarta na iya buƙatar tafiya hutu, tsallake waɗansu sassa, ko su dau tsawon lokaci a waɗansu sassa na musamman.

**Ya kamata a fitar da tsari na musamman game da zane-zanen su kansu kafin lokacin tattara bayanai (ko zartarwa)** sannan ta hanyar haɗa kai da abokan haɗin gwiwa a cikin al'umma. A waɗansu mahalli, zai fi dacewa a riƙe zane-zanen, a waɗansu lokuta kuwa, zai fi dacewa a mayar da su ga mahalarta ko a raba su ga al'ummomi. Ko ma wace dabara aka ɗauka, lafiyar mahalarta da kasancewarsu cikin aminci da tsaro dole ne su zaman abubuwan da aka fi la'akari da su.

## RESOLVE NETWORK

Bincike Mafi Kyau | Tsararrun Matakai | Ingantattun Dokoki Game da Hatsaniyar Ra'ayin Wuce Gona da Iri

www.resolvenet.org | @resolvenet

*Ra'ayoyin da aka bayyana a cikin wannan rubutu na marubutan ne. Ba dole ne su wakilci ra'ayoyin RESOLVE Network ba, ko abokan haɗin guiwar da aka ambata waɗanda suka taimakawa wajen wallafa wannan rubutu, ko Hukumar Zaman Lafiya ta Amurka, ko duk wata hukuma ta gwamnatin Amurka.*

UNITED STATES INSTITUTE OF PEACE
Making Peace Possible

RESOLVE na ƙarƙashin Hukumar Zaman Lafiya ta Amurka, tana ɗorawa a kan aikin Hukumar wanda ta shafi tsawon shekara goma tana yi, wanda ya shafi aiki tuƙuru ga yankunan da tashe-tashen hankula suka shafa.

USAID
FROM THE AMERICAN PEOPLE

RESOLVE na amfani da wannan dama wajen godiya ga Sashen Afirka na Hukumar Raya Kasa da Kasa ta Amurka (USAID) dangane da gudummawarta ga wannan rahoto da kuma Nazarin RESOLVE na Binciken Ɗaukar Darrusa Daga Hanyoyin Samar da Zaman Lafiya.